


A zamanin da can, dabbobi basu da kafafun tafiya. Dukan su jan ciki suke yi.




Mutane kaɗai keda ƙafafu, waɗan da Madugu ya basu.



Wata rana, Madugu ya ƙudurci bai wa kowace dabba ƙafafu. Ya sanar da su.




Dabbobin suka ce,
"Yana da kyau sosai
mu samu Ƙafafu."
Suka yi rawa da waƙa.




Dabbobin suka ce,
"Jan ciki yana yi masu wahala." Suna jin ciwo.



Da ranar ta zo,
Dabbobin suka je
gidan Madugu.
Dabbobin sun jeru
reras.



Ko wace dabba an
bata ƙafafuwa huɗu.
Tsuntsaye an basu
ƙafafuwa biyu..




Komai ya canza bayan
sun samu ƙafafu.
Wasu rawa don
murna. Wasu sun faɗi.



Sun je sun nuna wa mutane. Dabbobin suka ce, "Ba za mu ƙara jan ciki ba."



Ƙadandoniya ce ta zo daga ƙarshe.



Madugu ya ba
ƙadandoniya dukkan
ƙafafun da suka rage.



Ƙadandoniya cikin farin ciki sai ta ce, "Zan f kowa ce Dabba sauri."




Bayan ƙadandoniya ta taf, Maciji yazo yana roƙon Madugu ya bashi ƙafafu.



Madugu ya ce, "Na bayar da su duka." Maciji ya ce, "Nayi nauyin barci!"



Madugu ya duba ko
akwai sauran ƙafafun,
amma bai samu
ragowar ko ɗaya ba.



Madugu ya ce, "Ƙa yi haƙuri." Maciji ya koma gida ransa ɓace.